JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA ١٣ Jimada al- Ula, 1443

MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI 1٧ Disamba, 2021

(١)

## HARSHEN ALƘUR'ANI DA YANDA AKE KIYAYE KAI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Littafi ne da ayoyinsa suke dalla- dalla, abin karantawa da harshen Larabci ga mutanen da suke da ilimi)** [Fusilat: 3], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai harshe wani kwasfa ne da yake ƙunshe da ma'anoni da al'adu mabambanta, harshe ɗaya ne daga cikin ginshiƙan da suke gina ɗan Adam, suke kuma da tasiri wajen samuwarsa, duk wanda yake iya magana da harsuna biyu, to ya haɗa al'adu biyu kenan, duk wanda yake iya magana da harsuna uku, to yana da al'adu uku kenan, yana kuma karantar abubuwan da hankula masu yawa suka samar, amma duk da haka, harshen uwa shi ne ginshiƙi mafi muhimmanci wajen gina al'adar mutum, duk mutumin da bai san sirrorin harshensa ba, ba zai taɓa iya sanin haƙiƙanin al'adun wasu ba, balle ya yi ninƙaya a cikinsu.

Harshen Larabci yana da wata sifa mai matuƙar muhimmanci wadda da ita ne ya bambanta da saura, shi ne harshen Alƙur'ani mai girma da Hadisan Annabi masu daraja, lallai mu'ujizar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) mafi girma shi ne Alaƙur'ani mai girma da bayaninsa da sirrorinsa na harshe, da na bayani, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Lallai mun saukar da shi ne a matsayin abin karantawa da harshen Larabci,**

**ko za ku samu ku yi tunani na hankali)** [Yusuf: 2], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Kaman haka muka saukar da shi a matsayin abin karantawa da harshen Larabci..)** [Ɗaha: 113], haka ma Allah mabuwayin Sarki yana cewa: **(Alƙur'ani ne da ake karantawa da harshen Larabci, ba kuma a karkace yake ba, ko za su samu su ji tsoron Allah)** [Az- Zumar: 28], Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Kaman haka muka yi maka wahayin Alƙur'ani da harshen Larabci, saboda ka yi gargaɗi ga mutane garin Ummul Ƙura da waɗanda suke gefensa, ka kuma yi gargaɗi game da ranar taruwar da babu kokwanto a faruwarta)** [As- Shura: 7], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Da harshen Larabci bayyananne..)** [As- Shu'ara'i: 195], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Lallai mun saukar maku da littafin da akwai ambatonku a ciki, shin ba za ku yi hankali ba ne?!)** [Al Anbiya'i: 10].

Lallai Alƙur'ani mai girma ya riga ya haɗe tsakanin harshen Larabci da aiki da hankali, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai mun saukar da shi ne a matsayin abin karantawa da harshen Larabci, ko za ku samu ku yi tunani na hankali)** [Yusuf: 2], sai Musulmai suka tasirantu da Alƙur'ani, suka sanya hankalinsu suka yi tunani akansa, sakamakon haka sai suka samar da cigaban da babu mai iya musantawa, haka ma Allah ya haɗa tsakanin harshen Larabci da kira zuwa ga ilimi, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Littafi ne da ayoyinsa suke dalla-dalla, abin karantawa da harshen Larabci ga mutanen da suke da ilimi)** [Fusilat: 3], ya kuma kwaɗaitar zuwa ga neman ilimi, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Lallai mun buga wa mutane dukan misalai a cikin wannan Alƙur'anin ko za su samu su wa'aztu, Alƙur'ani ne da ake karantawa da harshen**

**Larabci, ba kuma a karkace yake ba, ko za su samu su ji tsoron Allah)** [Az Zumar: 27 - 28].

Babu wanda yake shakkar cewa ba zai yiwu a iya fahimtar addini da kyau, kuma ta ingantacciyar hanya, ko a samo hukunce- hukunce daga cikin littafin Ubangijinmu mai girma da buwaya, ko sunnar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ba, sai an fahimci harshen Larabci da kyau, kuma a gaban malamai, lallai harshe shi ne mabuɗin fahimtar addini, Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) yana cewa: A da ban fahimci ma'anar:

**{فَاطِرُ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ}**

ba har sai da wasu Larabawan ƙauye guda biyu suka zo suna rikici game da wata rijiya, sai ɗaya daga cikinsu ya ce:

**أنا فطرتُها،**

Yana nufin: **"Ni ne ya samar da ita"**, hasali ma malamai masana ilimin Usulul Fiƙhi, da masana Fiƙhu da sauransu sun sanya sanin harshen Larabci da kyau, da sanin abubuwan da ya ƙunsa a matsayin ɗaya daga cikin muhimman sharuɗɗan ijtihadi, alhairin Allah ya kai wa Hafiz Ibrahim a lokacin da yake magana da yawun harshen Larabci, yake cewa: **"Na gamsar da littafin Allah ta hanyar lafuzza da kuma manufofinsa, ban taɓa gazawa game da wata aya ko wa'azozi ba.. ta yaya a yau kuma za a ce na gaza wajen sifanta na'ura, ko samar da sunaye ga sababbin ƙere- ƙere? Ni ne fa kogin da a cikinsa yake ƙunshe da gwala-gwalai, ina ma a ce sun tambayi masu nutso game da kwasfofin zinare da suke ciki na?!".**

(٤)

Haka ma babu mai musunta cewa rashin sanin harshen Larabci da sanin ma'anoninsa, da kuma rashin zurfi wajen fahimtar Nassi da sanin abubuwan da suka rataya da shi, da kuma wadatuwa da doron nassi da zahirinsa ba tare da saninsa sani na diƙin- diƙin, da riskar sirrorin cikin ba, abu ne da yake yin sanadiyyar aukawa cikin manyan kura- kurai, ta ma yiwu mai yin haka ya auka cikin munanar fahimtar da za su iya kai wa zuwa ga halatta jinin mutane; saboda haka lallai fahimtar Alƙur'ani da da Sunna farali ne kuma wajibi, ba kuma sai samu ba sai ta hanyar karantar harshen Larabci, **duk kuwa abin da wajibi bai zai samu ba sai da shi, to shi ma ya zama wajibi**, Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: Ku koyi harshen Larabci, saboda yana cikin addininku, wata rana ya wuce ta wurin wasu mutane suna koyon harbi da kibiya, suna kuskure, sai ya nuna rashin jin daɗinsa da haka, sai suka ce:

"إنا قوم متعلمين"

Ma'ana: **"mu 'yan koyo ne"**, sai suka sanya wasali bisa a inda kamata ya yi ya zama rufa'a, sai (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Wallahi kuskuren da kuka yi a cikin harshenku ya fi mini zafi akan kuskuren da kuka yi wajen harba kibiya, Abdulmalik Bn Marwan (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: ku inganta harshenku, lallai wani bala'i zai iya auka wa wani mutum, sai ya aro tufafi da abin hawa, amma ba zai taɓa iya aron harshe ba, lallai kyawon mutum shi ne azancinsa.

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Babu shakka kan cewa lallai harshen Alƙur'ani shi ne ya tattara tarihin al'umma, ya kuma kiyaye shi, shi ne kuma yake ƙunshe da ginshiƙan tunani da al'adu a tsawon tarihi, shi ne kuma lamuni na wanzuwar al'umma da dawwamarta; lallai samuwar kowace al'umma daga cikin al'ummomi ya rataya ne da harshenta, idan harshen nata ya gushe, to ita ma ta gushe kenan, ta shiga cikin ɗimuwa a cikin al'adun wasu cikin al'ummomi; saboda haka, muhimmanta harshe babban alama ne da yake nuni zuwa ga muhimmata kai, da kuma bai wa kai kariya, harshe shi ne alamar da yake nuna haɗin kai, da daidaituwar manufa da tunani, kaman yanda harshe shi ne kwasfa ta al'ada mafi muhimmanci a cikin kowace al'umma da al'ada.

Lallai akwai buƙatar mu farka, mu kuma yi gwagwarmaya da duk wani yunƙurin narkar da mu a cikin wata al'ada, mu kuma yi aiki tuƙuru wajen ƙarfafa cigabanmu wajen fuskantar goguwar da take neman ta yagalgala mu, za mu yi haka ne ta hanyar muhimmanta harshenmu, da ba shi kulawa ta musamman, shi ne mabuɗin kawunanmu, yin tinƙaho da shi, yin tinƙaho ne da kawunanmu, hidimta masa kuma hidimta wa addini da ƙasa ne.

**Ya Allah Ubangijinmu ka kiyaye mana ƙasarmu daga dukan abin ƙi da sharri, da ma sauran ƙasashen duniya.**